[23/04, 14:54] +234 808 996 5176: 🏵🎗🏵🎗🏵🎗
*🐾YARO  DA KUDI*🐾
🏵🎗🏵🎗🏵🎗

✍🏻
*WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*Bissimillahi rahamanirrahim*

*Nafara da sunan Allah mai rahama mai Jin kai Allahu buwayi gagara Misali. Allah yanda kabani Ikon fara rubun littafin kasa na kammalashi lafiya*

👌🏻A RASHI

WANNAN LITTAFIN QAGAGENE DAGA NI BINTA  BANYI DAN WANI KO WATA BA WANDA YAGA YAYI DAIDAI DA YANAYIN RAYUWARSA TO A RASHIN SANI NE👌🏻

*Ban yadda wani ko wata ta juya min littafi ba batare da izini na Dan haka a lura*

💋Bakina bazai iya fadin irin godiyar da take cikin zuciyata ba Amma na barwa zuciyata komai tabbas nasan Akwai so na gaskiya a zuqatanku Ku kun San kan Ku ba sai na fadaba Allah ya bar kauna ta Dan Allah💋

*Iyayena Abin Alfaharina Allah yaja min da ranku yakara muku lafiya Ameen*👏🏻

🅿 1

Wani matashin yaro ne zaune cikin Wani haddaden falo  dashi da Abokanshi sun kaceme sai har gowa suke gefe guda kuma Abinci ne da Abinsa birjiki gasunan anci an barsu  !

"Yana zaune kan kujera cikin wasu kananun kaya da sukayi masa bala'in kyau  kafarshi daya kan daya kamar wani mace Hannusa riqe da *Sigari* yana busawa  da kangashi Kaga Dan duniya domin ida nunshi a Bude suke dudu shekarunsa baza su haura  24 ba!

Yanada kudi sosai domin kafatanin danginshi basusan wani Abu ba waishi talauci  "yan boko ne taimi  dukkanisu duk Wanda ya kwana yatashi A family nasu sai yayi kararun boko basu damu da yin kara tun Addini ba  sosai qalilan daga cikinsu ne suke mai da hankali suyi!!

To Shima *NASIR AL'HUSEN* yana cikin jerin waddanda basu damu da karatun Addini ba yafi mai da hankali a boko domin tun yana shekara Sha shida yake can America cikin turawa karatun boko ya samu shekara takwas a can Dan haka duk wasu munanan dabi'u a can ya dauko Abinshi. Idonshi idon Mata ne mutukar ya kyalla ido yaga mace mai kyau nan da nan zai rude zai iya kashe ko nawa ne a kanta domin samun biyan bukatarsa

Yana ta6a shaye shaye Amma baita shangiya ba har yanzu  suma kayan mayen sai sun fita yawace yawacensu da Abokai yakesha ko in zai nemi matanshi baya ta6a yadda yasha wacce zata bugar dashi dayawa masu tsada yake Amfani dasu

Yana 6oyewa iyayenshi duk a zatonsa basu gane ba tuntuni dadyn dinshi ya fahimce shi shi dai kwai yana masa Addu'a
Mom d'inshi kuwa Sam bata Fuskanci komai ba dake macece mai son yara kwata kwata batason laifinsa duk Abinda yayi dai dai ne!
Shiyasa suke dasawa dashi. Dan yana sakewa da ita sosai bakamar dady nashi ba!!

*MRS AHAMAD GWADABE CE*
💋💋💋💋💋💋

*INA TARE DAKU HAR KULLUM*
[23/04, 14:54] +234 808 996 5176: 🏵🎗🏵🎗🏵🎗
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵🎗🏵🎗🏵🎗

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿2*

Mom' dinshi ma'ai kaciyar Lafiya ce a sibiti" da kowane lokaci tana zuwa Aiki 'sabe rana dare shiyasa duk sanda zata je Aikin kwana yake tsula tsiyarshi a gidan. Dan mata yake kawo wa suyi Abinda suka ga dama dashi da Abonkanshi gashi yanada wata baiwa da Allah yayi masa na farin jini! Babu maza babu mata babu yara kanana babu manya kowa yasan *Nasir* sabida yawan kyautarshi da wasa da dariya domin mutum ne shi mai yawan fara'a yana sakewa da kowa a family nasa  sosai In kacire dady n shi gaisuwa ce kawai a tsakaninsu domin ko taro a ke irin na family bai zuwa sabida dandy dinshi ne shugaban taro to duk sanda yake gabatarwa a gurin a taron Sai yayiwa *Nasir* shagu6e A kan Yasan ya San Abinda yake Ai katawa a bayan fage shine dalilinda duk ranar daza a gabatar da taron yake kirkirar wani Abu domin yaki zuwa"

A kwai "yan mata Biyu Hasina da Mubina da suke mutuwar sonsa a family din Dan har fada suke da juna gami da gaba duk a kansa gashi sunayi shi Sam bai Sani ba su suke wahalar da Kansu domin shi a halin yanzu babu Maganar Aure yaruwarshi yake ci da tsinke!!

*wannan kenan*

********************

Wani Wanda suke kira da mansur shi yadawo kusa da *Nasir* ya zauna yana dariya kasa kasa yace yaya yau din kuwa zamu fitaa kasan Anyi sabuwar dauka!

Fuska yasaki kadan yace kai wasa ma kake Babah dole ne muje Ai muga ni Ammafa kasan ni bana son kananun yara nafi son manyan baby's  yadda zanjini a ciki ruwa tsun dum ko ina da bayani!
Hannu Mansur ya bashi suka tafa yace kai *NASS*
kana San kan har kar shegen Sama wai maye sirri ne sabida na lura "dakansu suke kawo kansu wataran basai ka nema ba"

Le6anshi nakasa yasa a baki yana wani Murmushi yace Sirri ai daga nine Abokina ni na yadda da kaina sabida nasan duk macen da ta dandana taji sai ta zo da kafadunta
Wata Mahaukaciyar dariya Masur yafara yana nuna *NASS* da Hannunsa yace kayi min daidai *YARO DA KUDI* nasan dama da kudi ko babu zasuzo ko su biya Ayi musu

Le6enshi dai yake tsotsa Wanda suka Dan rine kadan sabida zuqar *SIGARI* yana lumshe ido yace Ai hakkinsu ne dole in bawa ko wace shegiya ko zata zubar ni A kwai "yar iskar da ta isa ta siye ni karya take duk macan da Kaga na kwanta da ita A kwai Abinda na hango!!

*MUJE ZUWA*

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:55] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI🐾*
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿3*

Daya daga cikinsu mai suna Anwar yace kwarai kuwa *NASS* Nasan ka da idon gane gane Dan Allah taya ya kake gane mace mai tes  yaya sirrin yake ne Abokina ?

"Mikewa yayi yace babu Wani sirri baiwace kawai Allah yayi min kasan na karanchi mata kala kala So ganesu bazai min wata wahala ba son danake musu ne ma yasanya na tsaya na yi karatu a Kansu!
Yace bara in yi Wanka nafito mufi ta Yau A kwai casu sosai yafada gami da dukan kafar "Anwar din yana dariya!

Abdul latif dake zaune yana kallo bai tsoma baki n sa ba cikin maganar tasu sai yanzu yace Wallahi
*NASS* Karage So mata wai kai baka gajiya da yin sex kullum turawa sun 6ataka  Allah zan fadawa dady Abinda kake shukawa a bayan fage kai ko gudun cuta ba kayi!

"Kai Dan Iska rabu dani yaruwarka ko tawa An so matan nace an so matan shikkenan sai in zauna spam ya kashe ni bazan je in zubar ba  kaje kafadawa dadyn din in yaji yayi min Aure kowa ya huta!
Yafadi hakane sabida yasan dady nashi bayason yayi mishi Aure yanzu a cewarsa sai yakara hankali  tunda yanzu dai shekarunsa 24 so yake yayi kamar 27 sannan yasan ya fuskanci yaruwa kwata kwata dadyn shi basan yana bin mata ba yafi gazgata Dan shaye shayen da

yakeyi Wanda A halin da ake ci yanzu yake yaqi da ya rabashi dashi!

Abdul latif dai yaron kanin dadyn *NASIR* Tare suka taso dashi ya girmi Nasir din da "yan watanni Amma bazaka taba cewa ya girmeshi ba domin shi mai karamin jiki ne yayin da Nasir yake do go ga tsayi ga qiba Amma ba sosai jikinshi a murje kyakyawane sosai  Mayan kananun kaya da manyan takalma sosai in ka lura da wuyanshi har wata sakarka ce siririya ta gwall a makale Askin kanshi kuwa "'irin na Mawaka n kan kasar America ne yayi wani tozo a tsakiya gefe da gefe a aske anyi mishi wani irin Aski "yan yatsunshi kuwa wasu manya manyan Azirfa ce masu bala'in tsada Wanda a kai musu a do da daimon a jiki
Haka yake matsewa cikin kananun kaya dake bashi da rama wataran in ya yi wata shigar sai ka rantse da Allah 2pac ne tsowon Mawaqin nan na kasar A America idan "yan wulakanchin na kusa dashi dashi kuwa har Dan kwali yake dauraw(Ban Dana)
Yasa wasu Uban safunan Hannu in kaganshi sai ka rantse black America ne domin kwata kwata baiyi kama da "yan Najiria ba!

*WANNAN KENAN*

Abdul latif yace dukana zakayi ne naga kana wani zabura!!

Tsaki yaja yana yayi masa banza ya maida idonshi kan su Anwar yace"guys ku jirani Dan Allah in fito Ku rabu da wan can mashiriricin!!!

*MUJE ZUWA*

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:55] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿4*

Babu Abinda Abdul latif yace masa Dan inda sabo yariga yasaba da iskancin Nasir!

Ya kalli su Anwar da Abbas yace wallahi Ku lura da dunyar nan naga kwata kwata Ba kwa wannan lissafin duniya fa Ba matabbata ce kuma duk Abinda ka shuka shi zaka girba Ku dinga Sara kuna duba bakin gatari duk Abinda kayiwa Dan wani to tabbata sai an wa naka!!

Nunashi da hannu sukayi suna dariya Abbas yace Malam Alaramma wa'azi kake mana ne kome kai fa kafiye  Takawa nuna ma tsoron Allah zakayi kome?
Sunayi suna masa dariya tamkar sun samu mahaukaci sabon kamu!!

Girgiza kai kawai Abdul latif yayi yace ai duk kunyi Nisa bazaku ji kiran da nake yi muku!

Kai ya sayyadi A ramma ya isa haka Dan Allah cewar Anwar yaciga ba dacewa babu ruwanka damu ka wai ido ne naka Dan iska kawai munan dashi zai biyo sawunmu Amma yanzu yazo yanawa mutane wa'azi waishi mai tsoron Allah Mtsssssss!!

Mi kewa Abdul yayi domin fita yace Allah ya ki yayeni kuma da kukeyi Allah ya shirya minku babu India zan biku yawon iskanci Allah ya kiyaye hanya yayi ficewarsa daga falon!

Yana Fita Suka kyalkyale masa da dariya gami da tafawa Anwar yace dubeshi Dan Allah wai shi ustaz zaka biyo sawumu ne ai!

A haka Nasir yafito ya samesu suna tai wa Abdul iskanci!

Cikin wani irin taku Nasir din yakaro so inda suke  yana wani irin Abu irin nasu na birni !!
Da sauri Anwar ya dunqule hannusa suka dinga wani irin Abu da hannuwan nasu shi da Nass din suna Dariya hade da dukan kafadun su!!!

"Abbas yace  Kai Nass yaushe kahada wannan Wanka kwata kwata bansanka dasu bah!
Kaga yadda kayi kyau kuwa "Hande some "Lailai yau zaka hada go sulow mutumina!!

Yana Wani irin Abu irin nasu na nigogi gami da gyara wani tabkeken Agogo dake daure a hannusa mai bala'in tsada yace waddanan kayan ai sun Dade a ajiye ka wai banyi Amfani dasu bane!

"Kayi kyau sosai dole in kar6i kayannan nima in maqala "kasan Mutumi na ne 50 Cent na Lura

shigarshi ka hada!!

Dariya Nasir yayi yace kwarai kuwa ni har yanzu duk mawaqr A  America bani da gwani kamarshi kasan ya'iya raff"hippo)

Abbas yace a ganinka Ba!

Wasu Riga da wando ne jikin Nasir wandon iya gwuwa ne wani burgujeje yasha a do ajikinshi birjik da Alji wuna gaba da baya rigar kuwa me kamar vest ce mai kauri da yankakken hannu itama burgujejiya da photon wani tsohon mawaqin kasar America 50cent a jikinta tafkeke sai wasu iyayen sarkoki a wuyanshi sai sheqi suke da Wata shigiyar hana sallah mai bala'in tsada da yasa a kansa!

Humm Fadin tsadar takalimin da'ike sanye a qafarsa bata lokaci ne totally in zaka lissafa kudin wannan  kwalliyar Nasir sun tassama dubbannin daruruwa domin shi kanshi takalmin ya kai dubu Dari da hamsin!!

"Cikin Nishadi suka Fita daga part din nsa ya sanya key ya kulle!!

Wata Shegiyar mota suka Nufa samanta a bude kalarta jace sosai  tayi masifar haduwa dagani sabuwar zuwace domin bata baza gari Ba gashi dagani sai an sanya kudade masu nauyi za'a mallaketaa!!

Zama sukayi ciki kana Nasir yatashi motar hade da sakin waqar Mawaqiyar nan (Rihanna) tuni Harabar gurin ya karade da dukan sifiqa ji kake duff Duff!

Da Sauri Malm Yau mai gadi yatashi domin bude get ganin yadda Nasir ya fafaro motar kamar zai tashi sama!

Tana Zaune kan bai n ci kamar ko da yaushe takan fito ta zauna kusa da mahaifinta ta Dan tayashi hira!

Tunda ga Fitowarsu Nasir har shigarsu mota bata dauke idonta daga Kansu Ba tanajin wani irin mugun bakinciki ganin yadda suka yi shiga kamar Ba "ya"yan musulmai Ba
Ran tane yabaci ganin yadda Mahaifinta ya mike yana rawar jiki domin bude musu kofaa"

Daga yau ta dauki Alkawarin mutukar tananan bata tafi  skull ba zata dingaa bude musu get din!!!

*MUJE ZUWA*💋
[23/04, 14:55] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿️5*

Malam Ya'u nata kici kicin bude get da Sauri ta Mike takarasa gurin tafara kokarin tayashi budewa!
A tare suka bude get din ita dashi sannan ta matsa gefe guda tana Dan sauke nuffamfashi domin dai get din bana wasa bane!!
Abin Mamaki motar taga ta tsaya Nasir ya zuge glass din motar Fuskarsa a sake ya Mikwa malam Ya'u hannu yace Arrama barka da Safiya"
Shima malam Ya'u hannusa ya mikawa Nasir din cikin Mutmchi suka gaisa Malam Ya'u yace za'a fita ne Nasiru Don Allah A kula da duniyar nan ka rike sallah ka dinga yi kan lokacinta duk Abinda kake idan lokacinta yayi kabari kaje kayi!

In da Sabo Nasir yasaba da Wannan surutan da Malam Ya'u take masa indai zaifita sai ya tsayar dashi yana masa Wasu maganganu a cewarsa"

Dariya Nasir yayi kadan yana satar kallon inda take tsaye tayi Saurin dauke kai domin kwata kwata baya San su hada ido da yarinyar Sabida idonta kamar na mage ne kwayar idon blue yarinyar Kamar wata Al'jana Shiyasa in zasu hadu sau dubu baya gangancin kallonta Dan wani Sa'in in ya hada ido da'ita kwana yake da yini gabanshi na Faduwa yarasa gane wace irin Masifa CE wannan Shine dalilin da yasa ya daurawa yarinyar karan tsana!!

"Yace karkar kadamu Arrama zamu kiyaye in sha Allahu  A cigaba da Addu'a yafada yana kara tashin Motar a karo na biyu!!

Malam Ya'u ya matsa gefe yabashi hanya yana daga Masa Hannu tare da yimin shi Addu'oi iri iri gami da Fatan Alkairi!

Ranta A mutukar 6ace taje ta zauna kan bainci tana zumbura baki!

Ma Haifinnata yazo ya zauna kusa da ita yace yaya A kayi ne  Yarinyar kirki kina yimin magana banji Ba Mai A kace a siya a Makarantar!?

"Cikin Shagwaba tace wallahi Baba ina tausaya Maka in dai nayi kudi sai ka bar wannan Aikin qaskancin da kake yi zan sai mana gida mutashi daga Wannan!

Dariya Malam Ya'u yayi yana girgiza kai yace ta yaro kyau take bata karko Allah ya Amsa Addu'ar ki Maryam zan fison haka nima !!
Amma kisani Babu Abinda Alh' Huseen Zai nema ban mishi Ba A rayuwata Sabida mutum ne shi Dan Halak tun kafin A haifeki yayi min Hallicin da bazan ta6a man tawa Ba a rayuwata!!

********************
Asalin Malam Ya'u Malam Yau dai haifaffen kasar kamaru ne Ba fulatani ne tsantsan ko a can kasar tasu a cikin qwauye suke sosai shiyasa ko Kalmar A! Da Hausa basu sani bah!!

*MUJE ZUWA*
💋💋

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:55] +234 808 996 5176: 🏵🎗🏵🎗🏵🎗
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵🎗🏵🎗🏵🎗

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿6*

'A zahirin Gaskiya ya'u suna fama da kanta ta talauchi sai a wayi gari su rasa Abinda zasu saka a bakin salati  ga mahaifinsa karfinsa ya qare shannusa da yake kiwo dasu duk ya kadar da

wasu duk domin Asirinsu ya lullubu mahaifiyarshi ya Findu tana da lalaura ta rashin gani gashi kurma ce bataji sosai sai anyi magana da kyau sannan!

Tare suke fadi tashi da Maihafinsa da sauran "yan uwansa har ta kai takawo suka hana maihafin nasu fita kiwo sabida girma da yafara kamashi rannan suna tafiya shida "yan Uwansa ya kallesu yace cikin fillanchi nifa ina tunanin in bar garin nan zan fita nema ko Allah zai sa a dace Amma ina tunanin fadawa Baffah Ba lailai ne ya yadda bah"

Wani yayan shi jibo yace kayi tunani mai kyau Ya'u kasamu baffa kayi masa bayani watakila ta Amince kasan Arzikin bawa baya wuceshi kila wani Alkairin ne yake kiranka!
Yaci gaba dacewa kai yanzu idan kabar nan wane gari zaka tafi ko in ce wace kasa kake son zuwa domin naiman kudi!

"Ya'u yace zan tafi Najeria ne kawai naji Ana cewa cibiyar kasuwanchi ce  mussaman wata jaha a cikin jahohin Najeria mai suna Kano naji su "Ilu suna fadin Wai ko baka da ko sisi kashiga wannan jahar zaka samu Alkairi sannan zaka SHIGA kasuwanni kasan cewar tanada manyan kasuwanni zaka shiga kayi buge bugenka babu mai hanaka in kanada rabo sai kasamu uban gida da zai tallafa maka har ka tsaya da kafafunka" duk cikin fillanci suke magana!

Babban cikinsu yace kayi dabara nima sai naji ina sha'awar binka to Amma mu muna da iyali baza mu tafi gari yagari kamar wannan Ba mubarsu wqzai kular mana dasu da iyayenmu kai din dai dama dabaka da Aure kai Yagi Idacewa kaje din zan samu Baffah in yimasa bayani Sosaoi" Ya'u yaji dadin qarfin gwiwar da "yan Uwansa suka bashi yayi ta Farin ciki sosai!!

To koda Jibo yafadawa baffah qudirin Ya'u nabarin kasartasu ta gado Abin mamaki basu Sha wata wahalar shawo kanshi Ba yaAmince yace yaji dadi da hakan Allah yasa Alkairi ne yake kiransa yace dasu suka shanu biyu a kasuwa domin a bawa Ya'u kidin guziri da Abinda baza'arasa Ba Abinda yayi saura a hannushi sai yafara Sana'a ko ta turawa a baro ce!!

Batare da bata lokaci bah a kasiyar da Shanu a kahadawa Ya'u kudi ranka ta kaff Ana jiran ranar tafiya

A kwai Abokinsa ilu tare zasu tafi ilu yadan fi Ya'u wayewa yanaji Hausa kadan kadan kasancewarsa mutum ne mai kurda kurda Ba Lamar Ya'u Ba ya kanshiga cikin kasuwannin cikin garinnasu yayi buge bugensa to A nan yake Dan tsintar ya rirrika daban daban!

Allah buwayi gagara Misali kamar jira a ke su Ya'u subar wannan kauyen nasu Annoba ta sauka a garin ta Ambaliyar ruwa Wanda ta tafi da bukkokin Al'uma gami da rayukan jama'a Wanda kafatin dangi da iyayen Ya'u suka shafe kamar babu su a doran duniya Ruwa ya tafi dasu

*inna lillahi wa'inna ilaiyi raji'un*

*MUJE ZUWA*

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:56] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾

🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿️7*

Lokacin da labari ya iski su Ya'u sun shiga halin dimuwa da tashin hankali  To haka suka hakura suka fawwalawa Allah domin ko dasu kayi yunkurin koma grain nasu mutumin da yakawo musu labarin faruwar hakan yace ko sunje babu wanda zasu samu domin qauyen ya shafe waddanda suke da shauran shan ruwansu a duniya suna gadon Asibiti sannan gwamnnatin kasar tana Aiki a gurin!

Haka su Ya'u suka hakura suka cigaba da yiwa "iyayensu da "yan uwansu addu'ar samun rahamar Allah  suka cigaba da yawon buge buge cikin kasuwanni  kafin Hausa ta zauna bakin Ya'u sai da aka yara sannan yafara ji da mayarwa  Sukafara harkar sai da ruwa (garuwa)  suna bin Unguwanni sun samu Alkairi sosai da sosai suka samu suka kama hayar shago suna kwana ciki shida ilu rannan ilu yace mai zaihana mu shiga kasuwa ne da waddan kudin da muka Tara da na hannunka sai mu sari takalma murinqa turawa ko a baro ne! Ya'u yace hakan yayi kyau gobe idan Allah ya kaimu sai mufita da Wuri! Allah kasa mufara Asa'a
Allah mai iko A kwai wasu "yan shayeshaye dasuke makalewa jikin katangar gidan da su Ya'u

suka kama hayar shago  Ashe sunji duk Abinda suke cewa suka biyo dare suka kwashe kudin nan tas sai wayar gari sukayi suka babu kudi inda suka'aje Neman duniya basu gansu bah
*innalillahi wa'inna'illahi raji'u*
Kuka wurjajan ilu yake yakasa daurewa!
Shi ko Ya'u na zucci yake yana tabawa ilu hakuri Amma ina ilu yaki yin ta wakkali!!

Ilu yana kuka yace yanzu kai Ya'u wakake tunanin zai sace mana kudin nan naga kamar bakadamu Ba wai kai ko da hadin bakinka aka sace mana kudine!

Cikin Mamaki Ya'u yake kallon ilu yace haba ilu wannan wace irin magana kakeyi kudinka fa basukai yawan nawa kudin fa dawa kake tunanin zan hada baki wana Sani a nan garin Dan Allah kacire wannan zargin cikin zuciyarka!

Ilu yace babu wani zargi Ai gaskiyace gashi nan baka damu Ba kamar yadda na damu to waye zai shi go yayi mana sata tunda dakin A kullle yake wallahi Kaine ka dauke ko kasa a dauke sai bayan kwana biyu kafito dasu kace tarawa kayi!

Wani bakinci da bacin rai ne yakama Ya'u ganin yadda ilu ya hakikance yana shirya masa qazafi domin shine zai zargi ilun a kan sace kudin in hakane sabida nasa kudin sun nunka na shi yawa Amma dubi Abinda yake fitowa daga bakinshi Dan rashin tawakkali!!

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:56] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿8*

Haka ilu ya kwana yanawa Ya'u bala'i gami da bakaken mangaganu karshe Dai Ya'u da yagaji shima yafara mai da martani ganin cin mutuchin da Ilu yake masa

Haka suka cigabah da rayuwa babu mai kula da Dan uwansa in gari ya waye ko wanne zai fita har kokinsa gurin kwanciya ne kawai duke haduwa Ilu ya dauki Ya'u da gabah sosai yayinda Ya'u yake bin sa sannu sannu yana mamakin halin ilu na rashin tawakkalinsa Yana masa magana  shi domin  yafi shi hankali!

Wataran Ya'u ya fito da safe  domin tafiya cikin kasuwa sabida sun kwana da Aiki Sauri Sauri yake tafiya Cikin tsautsayi Yazo tsallaka titi wata mota ta kunnu kai ta yi gabah dashi!

Cikin  Sauri Mutumin dake cikin motar ya fito cikin tashin hankali yana wa drevar shi fada yace Na Hana irin wannan tukin ganganci  Nura wai mai yasa kake yin haka

Kafin Alhji huseen ya karasa gurin tuni Nura Drever ya je yadaga Ya'u yana masa sannu gami da duddubah jikinsa
Alhji ya karaso gurin yana fadi kamashi mutafi a sibiti a dubashi kana Neman ka jawo mana wanin tashin hankalin"

Ya'u ya mike da kafafunsa yana karkade jiki yace babu ciwo a jiki Alh kuyi tafiyarku haka nagode yafada cikin hausarsa da bata fita

Alh Huseen yace A'a dole zamuje a duba ka Aboki ka kwantar da hankalinka shiga mota mutafi

Shi ko Ya'u tsoro ne fall a zuciyarsa ganin Uban motan dake su ke ciki yace a yi haka yalla6e

Nura Drevar yace an yi angama Dan fillo ka kashiga mota babu Abinda zai same ka sai Alkairi

Babu yadda Ya'u ya iya haka ya shiga mota gabanshi na faduwa sanyi ne ya fara damunshi tuni yafara karkarwa Alh  huseen yace Nura maza kashe  AC din nan da sauri Nura ya cika Umarni Alhji ya kalli Ya'u yace meye sunan Malamin

Cikin nutsuwa Ya'u yace Zakari Ya'u sunana Alh

Masha Allah kai mutumin ina ne da'Alama Bako ne kai a nan ko ?

"Kwarai kuwa Alh Ni mutumin kasar Kamaru Yau wata Hudu a garin nan nafito nema Alh"

*kuyi hakuri dani*
💋💋

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:56] +234 808 996 5176: 🏵🎗🏵🎗🏵🎗
🏵🎗🏵🎗🏵🎗

Masha Allah Zakari Ya'u Allah yabada Abinda a kafito nema yanzu wace kasuwa kake zuwa ko in ce wane aiki kake yi ne?

Ko wane Aiki in yazo inayi Alh muna shiga kasuwa ni da Dan uwa Wanda mukazo tare muyi dako da Abinda ba'a rasa ba

Masha Allah haka A keson mutum mai himma zakari idan babu damuwa zan daukeka Aiki a gida Zaka dinga zama tare da Baban gida a bakin Get za Ku dinga lura da masu shige da fice ina fatan zaka Amince

Shiru Ya'u yayi yana sake sake cikin zuciyarsa

Murmushi Alh huseen yayi yace ko baka Aminta bane Malam Zakari"?

A'a Alh Na A mince Allah yasaka da Alkairi Allah yakara budi Amma zan gayawa Dan Uwana sabida shima yana Neman Aiki duk tare muke fadi tashi dashi"

Babu damuwa Ya'u Allah yashiga mana gaba ka Kwantar da Hankalinka dani domin ni tunda naganka naji ka kwanta min a raina Wallahi ina fatan duk manyanka sunanan lafiya?

Allahu A kabar Ai Allah yayi musu Rasuwa Alh kwananmu Uku a nan garin Annoba ta sauka a kyauyanmu ta barkewar ruwa wacce ta tafi da rayukan Al'uma da dama  cikin su har iyaye da

"yan Uwa

Allahu Akabar Hakika duk mutumin da ya mutu ta wannan tafarkin yayi shahada tabbas munji wannan labarin watannin baya da suka wuce Allah ya gafarta musu Dan Annabi

Ka kwanta da hankalinka dani ni zan riqe da Amana in Sha Allah

Ya'u yaji dadin karramarwar da Alh huseen yayi masa cikin zuciyarsa yana ta godewa Allah bakinshi yaki rufuwa yana ta godewa Alhji Huseen

To ko da Dr yadubah Ya'u babu Abinda ya sameshi sai "yar kujewa wacce ba'a rasa bah haka yahada masa magunguna kana suka fito

Alh yace Maza Nura ya kaishi ofis ganin lokaci yana Neman wucewa  bayan ya ajeshi ya kalli Ya'u dake cikin Mota a zaune yace yanzu Nura zai mayar da kai gida  kaje ka huta tukkuna ka bar maganar zuwa kasuwa idan Allah ya kaimu gobe Nura zai zo ya dauke ka ya kaika gidan nawa

Nagode Alh Allah yasaka da Alkairi

"Alh Huseen yaciro kudi Kimanin dubu Hudu zuwa biyar yabawa Ya'u yace kaci Abinci dasu zuwa gobe Allah yasawaqe

Sai godiya Ya'u yake bakinshi yaqi dai nawa sai da Alh yace masa ya'isa haka ya kalli  Nura yace kuje Kawai Allah ya stare

Cikin A zama Nura ya juya kan Mota domin cika Umarni Cikin Murmurshi Alh yadagawa Ya'u hannu yace A sauka lafiya Malam zakari Ya'u

Shima nasa hannun yake daga masa Cikin Farin ciki yana ta zubah godiya bakinshi yakasa dai nawa!

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:57] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*YARO DA KUDI*
🏵🎗🏵🎗🏵🎗

*WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿9*

Ko da Ya'u ya sanar da ilu halin da 'ake ciki babu Abinda yafito daga bakin ilu sai Wallahi kaje a ka siyar da kanka baburuwa ni bada sa hannu na kuma daka ke cewa ko zanzo muje gidan mutumin tare ni babu inda zani kaje kai garin kwadayinka zaka rasa ranka"

"Ya'u yace babu komai Amma yanda na lura da mutumin yana da imani bashi da mugun hali Dan da yana da mugun hali lokacin da ya bugeni zai ce da mai tukashi a motar suyi tafiyarsu Amma abin mamaki ya tsaya ya kaini Asibiti ya sai mun magunguna kaga ma kudin da yabani yace inci Abinci zuwa gobe"

Ganin irin kudin da Ya'u yafito dasu cikin Aljihunsa yasa gaban ilu faduwa domin a wancan zama in kudin masu yawa ne dadin dadawa kuma dukkanisu basu taba ruqe kudi irin wannan bah

Gaban ilu nafaduwa ya matsa can gefe yana kallon Ya'u yace kai kai Ya'u a INA kasamu wannan kudin Laillai anyi cinikin kan ka an baka kudin Wallahi kaima ban yadda dakai Ba Au da kai za'a hada baki a siyar dani ilu duk ya gigice sai daga murya yake yanaso yatara musu jama'a yacigabah da cewa Laillai dole kabar shagon nan ko in Tona maka Asiri Wallahi bantaba zaton haka halinka yake bah Ya'u

Ganin yadda ilu yake tada jijiyar wuya tasa Ya'u yafara kwantar da Murya yace ka tsaya ka fahimceni ilu babu cuta a tsakinana dakai ka tsaya murafawa kanmu Asiri mutumin nan zai tai makemu ne bashi da niyyar cutarmu

INa! ilu ya kasa fahimatr Ya'u Dan haka baran baran sukayi ganin yadda yake Dada wayar masa da kai yakasa fahimta sai shima yabude masa wuta was he gari baran baran suka rabu lokacin da Nura Drevar yazo daukarsa babu irin sharrin da mugun Alkaba'in da ilu bai jefi Ya'u dashi duk yanajinsa yai masa banza koda suka bar Unguwar Nura Drevar ya kalli shi yace wai yaya kuke da wancan mutumin ne Malam Ya'u naga sai zaginka yake

Ajiyar zuciya Yayi yace Shine Abokin tafiyartawa Wanda nake gayawa Alhji jiya babu yadda banyi dashi Ba ya ki fahimtata Dariya Nura yayi kadan yace ai sai ka rabudashi tunda yaqi ya gane bashi da rabo ne kawai

Allah ya sawaqe shine Abinda ya'u yace ka wai yaja bakinshi yayi shiru yana mamakin irin rashin mutumchin ilu!

Alhj Huseen suka dai yake jira a kimtse yake domin tafiya gurin Aiki ko dasuka karaso gidan Ya'u ya tsorata ganin wasu irin dogayen gidaje masu kyau ya lura tunda suka shi go Unguwar ko wane gida bana wasa shi kanshi kofar gidan Alhji Huseen din Police ne a zaune kan banci Gabanshi yafadi Amma kawai sai yafara Addu'a cikin zuciyarsa karfa maganar ilu tazama gaskiya!

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:57] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿10*

Ko da Malam Ya'u yashiga gidan di maucewa yayi kanshi tafara juya masa jin haushin karnuka sun cija gidan sakamakon ganin bakuwar fuska da sukayi sai Da Alhji yasa ka janyesu sannan a kasamu lafiya da jikin Ya'u sukazo suna shanshanawa kamar zasu cijeshi
Nan Alhji huseen ya gabatar da Ya'u ga ma'aikatan gidan yace Dan gidane shi yayiwa babangida bayanin zai dinga zama tare dashi bakin Get kafin ya samar masa Abinyi Wani katon daki nan Alhji ya nunawa Ya'u yace yashiga ya aje kayanshi ciki ya kwantar da hankalunshi Allah ne ya hadusu cinshi da shanshi duk yana hannushi kar ya damu a kwai Wanda yake dafa musu Abinci isu isu mai rai da lafiya A kwan kankace kwabo Ya'u ya murmure ya saba da kowa na gidan Kulum suna tare da Babangida jininsu ya hadu sosai dake baban gida mutumin kirki ne gashi dama Ba yaro bane shi ya kusa haifar Ya'u ma shiyasa yakesonshi sabida bashida da

namiji Cikin hukuncin Ubangiji soyyaya mai karfi ta kullu tsakanin Ya'u da yarunyar Babangida wato Suwaibah  yarinyace nitsatsiya shiyasa ko lokacin da Alh Huseen ya ji labarin yayi Farinciki sosai shi yayi walicin Ya'u yashige gabah a ka daura Auran babu Abinda bai yimishi Ba nagata bangaran sa daban komai ya zuba masa na more rayuwa

Lokacin Nasir shekarunsa Sha biyu a duniya Jininshi ya hadu da Ya'u I Dan babu skull haka zai tafi bakin get ya zauna tsakiyarsu suy ta bashi labari yana dariya musamman in Ya'u na bashi labarin garinsu da yanda suke rayuwarsu a saukake  da irin cimarsu duk da karanchin shekarunsa a wancan lokacin ya fahimchi Ya'u bashi da kowa a duniya sai dady dinshi dake Nasir yana da tausayi da zuciyar mai saurin kuka idan Ya'u nabashi labari bakar wuyar da sukesha dashi da "yan uwansa sai yaita tsiyayar da hawaye nan suka shaqo sosai da Ya'u idan dady dinshi yadawo daga Aiki yatar dashi gurinsu yanajin dadi dama yanaso yaron yataso da zuciyar da tausayin nakasa dashi bayason danshi yatashi da girmankai irin nawasu yaran masu kudi
Momy dinshi ko babu Abinda yadameta ita ma duk Abinda yaronta take so tanaso domin bata son Abinda zai bakanta ran sa ko kadan

Bashi da gurin Zuwa sai bangarn Ya'u idan Suwaibah tayi girginsu na gargajiya ya zauna yaci tun bai iya cibah ya koya haka zai ta santa Aunty nashi namasa dariya domin Aunty yake cemata

Lokacin da Farga Suwaibah na da ciki Munna yayi tayi kasancewar shi daya JAL babu wa babu kwanwa sakamakon tsarin iyalin da Mom dinshi take ita lailai bazata haihu bah sabida Aikinta

Yace Auntyna Allah yasa ki hafarmana baby girl Allah ina son baby ni dai

Duk lokacin da yayi mata irin wannan maganar dariya take tace Nasir kenan to Allah yasa ya Amshi addu'arka!!

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:57] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Omar
(MANAN ABDUL WAHABU)

*🅿11*

Dariya ya kanyi a lokacin yace duk ran da kika samar nin baby hannun Mom dina zata dawo gaba daya zaki bar mana ita taxama tamu dariya kawai Suwaibah takeyi a lokacin in taji Nasir na fadin haka sai tai ta biye masa

Ranar da suwaibah ta haihu Nasir bayanan yana skull ko da yadawo tunda ga bakin get Babangida yayi mishi Albishir kai tsaye bangaransu Ya'u ya nufa Fuskarsa sake yana Murna ko ya tsaya ya tambayeshi namiji ko mace yana shiga ya hau kwalawa Aunty tashi kira yace Aunty Allah yasa baby girl ce Allah ya Amshi Addu'a ta bata falon a lokacin da yake maaganar tana toilet sai  wata dattijowa yayar mahaifiyarta tana zaune dauke da jaririya A hannu bayan taga mata Wanka!
Tace A,a "yan samari shigo mana ai tana bandaki tana Wanka zo ka dauki jinjinniyar gata nan tubarkallah da sauri yakarasa falon Hannushi yana karkarwa ya karbi baby sai sakin murmushi yake  bakinshi ya daura a fuskarata a lamun kiss yayi mata ya kura mata ido yana kallo yarinyar kyakkyawa yafada cikin ransa Abin mamaki babyn ta bude ido sukai ido hudu da sauri ya dauke idonshi gabansa na faduwa wannan wane irin ido ne Anya wannan baby n mutum ce yake fada ci kin zuciyarsa  ya qara kallonta a karo na biyu still idon baby a bude yake  Sai jikinshi yafara rawa domin shi dai bai taba ganin "Dan hausawa da irin wannan idon Ba ko a turawa ma sai an tona za'samu duk da ce wa skull dinsu turawa ne mafi a kasarin malamansu ya Sabah kallon irin wannan hallitar Amma fa na wannan baby yayi yawa kwayar ido blue Allah mai iko duk da take jaririya baiwar da Allah yayi mata tafito sosai domin Ba kowace hallita Allah yakewa wannan baiwar bah
Da sauri ya mika ta ga wannan dattijiwar yamike yace  idan Aunty tafito kice mata Nasir yazo yaga baby Allah yaraya ya fice yana mamaki
Ko da Aunty tafito take tambayar waye yazo  yakumbonta tace wani yaro ne dan kyakykyawa da Alama shine Nasir din dakike fada yaron masu gidan
Dan yace a cemiki Nasir ne zai dawo in an jima
Dariya Aunty tayi tace shine mana yadauki baby ne?
"Eh ya dauketa Amma kamar a tsorace da Alama bai saba da daukar jirajirai bah
Kwarai kuwa bashi da wa ko qanwa shiyasa ya kallafa rai ai na haifi mace wai zai kawa mom dinshi na sake haifo wata dariya yakumbo tasa tace ai suncancanci Abasu duk abinda suka nema sai kicika Alkawari tunda kin dauka" dariya Aunty tasa tace Nasir Rigima kenan nan da anjima zakiga ya dawo

To Abin Mamaki har bayan isha babu Nasir babu labarinsa Aunty tashiga mamaki cikin ranta tace duk yadda a kai babu lafiya tasan da tuni ya shi go!

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:57] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*YARO DA KUDI*
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Omar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿️12*

Har gari ya waye babu labarin Nasir sai da zai tafi skull ne ma yashiga ko zama baiyi Ba daga tsaye suka gaisa da Aunty nashi tace jiya nai tajiranka ka dawo naji shiru lokacin da kashigo ina ban daki wallahi wai harkagama dokin baby ne kashigo ka dauketa
Dariya yayi kan yana dauke Fuska yace yanzu sauri nake aunty in na dawo na dauke ta Ammafa baby naki tana da kyau sosai Allah ya rayata Aunty tace babyn ka dai ko kafasa dauka na bar ma girgiza kai yayi yana ya mutse fuska yace Babar miki a barki aunty kwata kwata batayi min Ba in kin samu wata na dauka yafada babu Abinda yadameshi da yake daman can shi bashi da rufa rufa ko munafurchi shiyasa ba'agulma a gabanshi Dan Wanda yayi gulma a gabanshi sha'Allahu mutumin da'akai yi dashi na zuwa gurin zai fada mishi ya kuma nuna Wanda yayi dashi yana dariya shiyasa ko a skull a bokananshi suke shakkarsa sabida Fayyace gaskiya komai dacinta yana da kirki sosai gami da Fara'a yana da farin jin mutane mussaman "yan mata gashi da kyauta bai raina talaka a yanda yake haka duk juma'a sai yabi massalan juma'a yarabawa Al'majirai sadaqa na kudi da Abinchi da tufafi shidai kawai barshi da mugayen halayenshi Wanda Allah ya jarrabeshi dasu

Cikin Mamaki Aunty tace haka zamuyi da kai Dan gidana meye laifin wannan baby nawa yace bata da Laifi Aunty baby kin tayi kyau wallahi kawai idonta ne banaso
Dariya Aunty tasa tace Nasir kenan to Ai shikkenan. Allah yabani wata babyn nayi maka Alkawarin baka ita har'abada sakin Fuska yayi yace OK Aunty na godiya nake bari in wuce. In tafi kar inyi latti Auty tace to Allah ya tsare yabada Abinda a katafi nema
Amin yace yasa kai yafice daga dakin cikin ransa haka ka wai yaji baya son kallon babyn Aunty sai yaji yana tsanarta a zuciyarsa yace anya wannan "yar Ba "yar ruwa bace aunty ta haifa farinta yayi yawa idan ko babu daya to tabbabs zai fadawa Arrama Ya'u yakaita likita ya dubata batada cikkakiyar lafiya

A kwan haka a kayi bayan yadawo daga skull da yamma yaje yasamu Arrama 'Ya'u dake haka yake cemasa sabida yawan wa'azin dayake masa lokaci zuwa lokaci shine kawai yake cemasa

Arrama ammafa bata iskancibah cikin sigar mutumci
Yace mai zai hana a kira Doctor ya dubah baby naga kamar batada lafiya ne idonta kamar Ba daidai yake Ba

Dariya Abun yabawa malam Ya'u yace ya'Asalin ba'a daidai yake Ba Nasiru. Shiru nasir yayi yana ya mutse fuska Malam Ya'u yacigaba dacewa ai haka hallitar idonta take mahaifiyata ta gado ai yadda idon mahaifiyata yake har yafi na Maryam din
Kallonsa Nasir yayi yace Sunanta Maryam Ashe?!!

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:58] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿️13*

Eh Ai tun jiya nayi mata hudubah da sunan maihafiya ne.
Ayya sunan Mom dina ne fa Nasir yafada fuskarsa a sake Malam Ya'u yace masha Allah kaga yarinya ta ci sunan kakaninta Allah ta rayata shine Abinda Nasir yace kawai ya ciga da cewa yau saura wata biyu fa in tafi America a can zan qarasa karatuna Cikin fatin ciki Malam Ya'u yace Allah yabada sa'a Nasiru yabada Abinda a katafi naima Dan Allah idan kaje ka kula da tarbiyar ka kar ka dauki dabi'un "yayan Nasara Allah ya tsare mana ka.Nasir yace karkadamu Alaramma in Sha Allahu zamu kiyaye a dai tayamu da adu'a a wan can lokacin idan Nasir yana maka magana sai ka rantse yayi shekaru ashirin sabida nutsuwarsa da yadda yake fitar da lafazi cikin hikima,
Lokaci n da Mom din Nasir taga babyn da Suwaibah ta haifa taji tana kaunar yarinyar Karin farin cikinta jin sunanta a kasawa yarinyar Dan haka shatara ta arziqi ta hadowa baby da uwar ta duk cewar Momyn bata da sakin Fuska da Jan mutane Amma darajar wannan baby yasa tashiga har bangaran su ya'u ta Abin Arziqinta tace ita tanason baby in zasu bata dariya Ya'u yayi yace ai dama takice Hajiya tuntuni Nasir ya karbar miki ko yanzu kikeso sai ki dauka Momy tayi murmushi tace A'a a dai bari tayi kwari tukkuna taga ma karbar nonon mahaifiyarta sannan sai in karba idan na karbeta yanzu yaya zanyi da Aiki na.
Kwarai kuwa hakane inji malam Ya'u yace to Allah ya kaimu lokaci Nan Momy ta tafi ta barsu suna tattauna maganar Ya'u yace ni mai mutannan zasu nema a duniya in hanasu mutukar ina dashi zan basu rai nane kawai bazan iya basu bah Suwaiba tace kwarai kuwa ai duk inda

mutanan kwarai suke sun kai sosai.

Kafin suyi Ar'bain Baby Maryam tayi wata irin qiba yarinyar tahada uban kyau kamar "yar turai ko Larabawa  a gurin Momy take wuni duk randa babu Aiki duk sanda Nasir ya shi go ya tadda ita A hannu Momy sai yace Momy Wannan Yarinyar kika dauko ? Momy tace gata kuwa kana gani My son Wallahi haka kawai nake son ta Yakan ta6e baki a wancan Lokacin yace kinga ni ko Momy Sam yarinyar batai min Ba Wallahi dariya Momyn take a lokacin tace kai yarona wannan baby n ai tana da kyau maiye laifinta. Daga kafada yakeyi yace babu ruwana da kyanta Momy kune kuke ganinshi yayi wucewarsa ciki har sai Momy ta mayar da ita zai fito yasake suyi hira da ita Sautari zai shigo ya tadda 'ita a bedroom din Momy kwance kan bed tana kuka in Momy na toilet haka zai tabe baki ya juya yafita baya ma karasowa dakin balle ta sa ran zai dauketa.

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:58] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿️14*

Watan Maryam Uku a duniya Nasir ya tafi America  karatu tafiyar da ta sauya masa rayuwa ta sauya masa kyawawan halayensa  yaje ya hadu da Abokai "yan "yan masu kudi Sosai da turawa su ka koya masa shaye shaye da Neman mata da duk wasu ta'adu na Nasara Abu daya zai ce ya riqe Wanda Allah ya tai makeshi bai yarba sallah ko da Ba a lokacinta bane yanayi baya bari ya kwanta baiyi Ba sai da yafara hankali ne yake yakice komai idan lokacin sallahr yayi yaje yayi sai wata baiwa da Allah yayi masa ta a zumin litinin da Alhamis bai yar Ba domin tun yana gida yakeyi tare da Malam Ya'u  to Abin ikon Allah bai dai naba duk shagalarsa ranar littinin da Alhamis sai yayi yake jin dadi,
Shekararshi takwas a can yadawo gida domin Hutu kafin ya koma ya cikashe shakuru hudu Fannin duk wata matsala da take damun mata ya ke karanta  Sosai ya ke binkice a kan

Matsololin da mata ke Fuskanta ta kowane 6angare kama daga gurin haihuwa gurin daukar ciki sankar Nono sanyin Mahaifa; Sanyi Mara; da shi kanshi HedeQuaetar din Babu Abinda baiyi binkice a kai Ba shiyasa yasan mata iri iri yake yi musu kallon Nasanku ciki da bai kamar yadda yafada Ba ko wace mace yake kwanciya da ita sai ya hango wani Cabin;
Lokacin da yazo gida Maryam tana shekara Tara a Duniya. Yayi mamakin girman Yarinyar sai bai CE komai Ba ko ya shiga bangaran Aunty tashi yasha tar6a sosai ta dinga INA a saka INA a je dashi tayi mishi girki na Mussaman ta aje gabanshi yayi murmushi yace Aunty na Abinci nan yayi yawa fa .tace kaci kabar saura Nasir Lailai girma yazo kaga yanda kazama wani kato kuwa mai turawan suke baka haka,? Yace babu komai Aunty  yanzu yaranki nawa ga wani boy nan shima naki ne yafada ya na nuna wani yaro dake kwance kan kujera bazai wuce wata biyar Ba, Dariya Aunty tayi tana zubah masa Abinci tace Nasir junior kenan ai ta kwaranka ne sunanka a sa bayan tafiyar nasamu yara UK' suna makaranta tare da yayarsu yanzu zaka gansu ai lokacin tashinsu yayi,

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:58] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿15*

A kwan kafin ta rufe baki sai ga Maryam tare da kannata sun shigo cikin kayan makaranta Nafi'u shine yake bin Maryam sai Miftahu ya kasance ita ce mace kawai a cikinsu Nasir yayi mamakin girman Yarinyar Kallo guda yayi mata ya dauke kai  Amma yayi mamakin ganin yanayi idontan nata ya Dan rissina Ba kamar tana jariri yaba Amma fa yananan da kalarsa bai sauya Ba  Aunty tace gaka "yan halak Ba dama yanzu nake CE maka zasu shigo. Gyara zama yayi yace Masha Allah Aunty na kin Tara basawa Haka Ashe babu baby girl dina Dariya Aunty tayi tace Allah bai kawo Ba Nasir ka ganta kenan Maryam yace naganta Aunty ta girma yarinyar gaskiya dariya Aunty tayi tace haka kowa yake cewa Sam batayo jikin Fulani Ba ita kam tana da rusheshen jiki Masha Allah  ta kalli su Maryam da suke tsaye suna kallon Nasir kamar sun sami Tvi suna mamaki waye wannan domin su kam basu ta6a yin baqo haddade Dan gayu irin shi domin Fatarshi ma Abin kalloce sabida gogewa jikinshi kwata kwata babu datti yana sanye cikin qananun kaya As'useal sai murmushi yake musu  Aunty tace kai Nafi'u kai ne kullum mai tambaya ta waye Uncle Nasr yau dai gashi nan a gabanka kun tsaya kuna kallon mutane babu gaisuwa har dake da girmanki tafada tana harararta. Washe baki Nafi'u yayi yakara sa kusa da

Nasir ya tsuguna yace sannu Uncle ya hanya kullum Aunty na bamu labarin ka da kirkinka Sai naji nima ina sonka ina son ganinka kullum sai nasa Aunty tayi min labarinka. Dariya Nasir yasa ganin yadda Nafi'u yake zubah sai kace wata tsohowar radio sai kawai ya daukeshi ya daura saman cinyarshi yace yayi boy Naji dadi nima ina sonka daga yau kazama Abokina mu daura ya mika masa ya tsansa daya da sauri ya sanya nasa suka makale da juna suna dariya Nasir nayi mishi irin Gaisuwarsu ta Nigogi da hannu shima A she ya iya sakamakon kalla da sukeyi a TV ganin haka yasa Miftahu tawowa shima yana Dariya wai shima sai Nasir yayi mishi irin Abinda suke da Yayanshi Nafi'u Aunty ko sai dariya take musu kan kace kwabo Nasir ya zage sai kyalkyala  dariya yake dama shi A kwai San yara ko a can ma haka yake 6ata lokaccinshi cikiin "yayan turawa suyi ta wassanni
Qaramin Hijab din dake wuyanta tacire ta zauna kusa da Aunty   ta'aje Jakarta kusa   da ita cikin sanyi Muryarta tace Aunty  wan an  ne Uncle  din dama?
[23/04, 14:58] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🎗️🏵️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿️16*

Aunty tace Shima Maryam gashi nan kina wata takwas ya tafi karatu can kasar waje gashi nan yazo Hutu zai koma Amma  Cikin Sanyi muryarta dai tace Uncle ina kwana kazo Lafiya ya hanya? Duk lokaci guda tayi mishi wannan tambayar yana can yana wasa dasu Nafi'u ya tsin kayi Muryarta a Dan sakaye ya dago kai Ya kalleta sai kuma ya yi saurin Mai da kansa kansu Nafi'u yace Lafiya lau Na sameku Lafiya Maryam? Dake yarinyar tana da wayyayan kai tace lafiya Lou Uncle. Daga bai ce mata kala ba suka cigaba da shirmansu shi dasu Nafi'u gefe guda kuma yana satar kallonta ganin yadda ta tube hijab babu Abinda ya dauki hankalinshi jikinta sai kyawun fatar ta da Wuyanta domin Maryam dai irin Masu cikkaken jiki ce bata da rama ko daya wuyanta har wani guru yayi Fatar luwai luwai tamkar wacce take rayuwa a kasashen waje Cikin zuciyarsa yace Ammafa yarinyar tana da kyan jiki da da ni fatarta zatayi Laushi sosai Wata zuciyar tace masa bama Fata Ba kadai wancan gurin na zaiyi taushi sosai tabbas za'a sameshi a cike Dam domin duk wasu A lamu ya hango a Dan kallon da yayi mata na Munti daya kar Ku manta dama nace daku Nasir Fanni Mata yake karanta da Binkice a kansu Dan haka gane kalar ko wace mace bazai masa wahala ba , Ya Mike yana kallon Aunty yace zan Dan shiga in kwanta Aunty Nagode Tace A,a ai bakici Abincin bah ko daya Murmushi yayi yace baki lura bane lokacin da naci Amma ki aje min idan an jima zanshigo in dauka Mikewa Aunty tayi tace a,a Ba zai haka Ba bara Maryam tabi ka dashi kawai da zafinsa kafi sakewa kaci nan fitinnanun yaran nan sun hanaka kaci  Yana kallon A gogo dake daure hannunsa Mai wata irin sarqa yace

OK Auntyna babu komai  nagode Momy ma tanasan yanzu tana kan hanya time din da wowarta daga gurin Aiki yayi. Eh Ai kam yau juma'a bata dadewa take dawowa Ai tana ma kokari Aunty tafada tana harhada kayan Abinci cikin wani kwando mai kyau  Shi kam Nasir tuni ya fita daga bangar Dan Ba zai iya zama jiran yarinyar bah  Aunty tace Maza bi bayanshi da Abincin kinga ko Uniporm dinki Baki cire Ba kin tsaya shirme Maza ki dawo kin San a kwai isilamiyya ko Karbar kayan Abinci n tayi da Sauri tabi bayanshi INA! Ai tuni Nasir ya shige part dinsa  Sai ta dinga diri diri dan bata San in da yayi Ba tafi minti biyar a gurin a tsaya kamar ta koma da Abincin sai kawai ta karasa can bakin Get gurin Kakanta Baban Gida da Mahaifinta  tsakanin Bakin Get din da Ai nihin cikin gidan A kwai "yar tafiya gaskiya tunda gidan Ba nawasa bane domain  har kwalta ce a shimfide a wasu guraran .tana ajiyar zuciya takarasa gurinsu Malam Ya'u na ganinta yace ina zakije da kayan Hannuki  ? A Nutse tace Aunty CE tace in kai wa Wani Nasir tace nabi bayanshi gashi ban San inda ya shiga kafin Malam  Ya'u yace komai Baban gida ya mike yana dariya yace muje in nuna miki gurinshi sokowa kawai nama Fasa auran dake tunda Ba kya ganewa"

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:59] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🎗️🏵️
*YARO DA KUDI*
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿️17*

Dariya tayi tana sun kuyar da kai Dan idan da sabo tasaba da irin wannan tsokanar da Baban gida yake mata na kaka da jika,

Part din Nasir ya Nuna mata yace ki shiga yana ciki kinji ko  Tace to" Shi kuma ya juya ya koma Bakin Get din,

Tafi minti goma tana Aikin buga kofar dakinshi nashi shiru ba'abude Ba cikin gajiya ta zauna gefe tanaji kamar ta koma kawai wata zuciyar tasa ta daukar dutse ta fara bubbuga kofar dashi da qarfin gaske'

A hargitse Nasir yafito daga toilet daga shi sai gajeran wando jikinshi duk kumfa yana Fadin Wane Mahaukacin ne yake min wannan Dan iskan bugun kofar tamkar zai fasa min kune Dan

iskanci ,shi duk a zatonshi irin Abokananshi na nane suka fara zuwa su dameshi jin cewar ya shigo kasar , kan yabude kofar sai mita yake yace ko waye basai ya kirani a waya ba meye amfanin Wayar tawa Mtsssss

Yana bude kofar yayi Arba da Maryam tsaye hannuta riqe da kwandon kayan Abinci Fuskarta ta nuna Alamun kosawa

Shi har ga Allah ya Manta da cewar Aunty tace yarinyar tabiyo shi da Abinci Wallahi sabida haka Wani banzan kallo yabi ta dashi yana ta6e baki yace ke wace irin daqiqiyar yarinyace iyi zakizo kinawa mutane bugu irin na Mahaukata  Sabida gidadanchi irin naki

Kallonsa Maryam take cikin Mamaki sabida yadda yake yabata Mamaki ganin yadda yanzu nan a gurunsu yake ta dariya da wasa dasu Na'fiu Amma dubi yanzu yana kokarin zaginta,

Dake yarinya ce mai sanyin Hali sai tace dama Aunty ce tace in kawo maka Abinci Uncle kayi hakuri,"

Mtssss yaja yashige cikin dakin ya barta nan tsaye , ganin ya tafi ya barta sai kawai ta ajiye kwandon nan tayi nufin fita ranta a 6ace duk da take yarinya bata kaunar mutum mai wulakanci tana da gudun "yayan masu kudi sosai Dan ko A skull dinsu bata sakewa dasu kasancewar duk makarantar babu Dan talaka makarantace ta "yayan wane da wane Dan Alhji Huseen ne duk yake daukar nauyinsu ita da qannata,

Cikin tsawa yace ke mai kama da jinsun ifiritu dawo nan ki kwashe kayan Abinciki da dai bake kika kawo min sai inci, Ni Wallahi tsoro kike bani maza fice min daga daki yafada yana dauke idonshi a kanta lokacin da ta Joyo Cikin Mamaki Maryam take duk da yarintarta a lokacin bai hana ta Fahimtar meye ma'anar sunan ifiritu yake Nufi Ba, jikinta a sanyaye ta dawo da nufi kwashe kayan, sai kuma ya caja shawara  yace ke barshi ma nafasa  Fice min daga daki duk randa nakara ganin kafarki cikin dakinan sai nasa su Rambo sun cakalkalamin Namanki yana Nufin karnikan su na gidan,

Simi Simi Maryam tafice daga dakin kamar tayi kuka

Binta yayi da kallo lokacin datake kokarin fita daga dakin a Filice yace haka kawai kisanya ni Mafarkai da Faduwar gaba babu gaira babu dalili ki cuceni

Abinda yasa ya hanata mayar da Abincin yasan dole ran Auntynsa ya 6aci shiyasa basa haka da Auntynsa ko bazaici Abu Ba in tabashi ya kan qar6a ne kawai domin yafaranta mata,

*gaskiya bana samun commet a wannan book ko in dai nayi muku*😞🤓

*MRS AHAMAD GWADABE*
[23/04, 14:59] +234 808 996 5176: 🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️
*🐾YARO DA KUDI*🐾
🏵️🎗️🏵️🎗️🏵️🎗️

*✍🏻WRITTEN BY*
Binta Umar
(MAMAN ABDUL WAHABU)

*🅿️18*

